





Mudi da Tanko abokan juna ne masu sha'awar guje-guje. Kullum suna guje-guje tare.




Wata rana, Tanko yace, ''Bari mu yi tsere a cikin Nahiyarmu. Bari muyi tsere domin goyon bayan haɗin kan Afrika!" "Mu taf!" Mudi ya amsa.



Sun yanke shawarar ɗaukar ftilar haɗin kai a tafyarsu. Sun fara tseren daga Kudu, a birnin Kef.





Daga Afrika ta Kudu sun bi ta gaɓar kogi ta yamma. Sun bi ta Kasashen Namibiya, Angola, Haɗaɗɗiyar Daular Kongo, Kongo da Kamaru. Sun huta a Abuja.




'Yan tseren Afrika ta yamma sun haɗu da abokansu na Nijeriya. Sun ci gaba tare, ta bin kogin Neja zuwa yamma.



Yanayin yashin ƙasar Mali ya basu wahalar ci gaba da tseren. Mudi shi ne gwarzo daga cikin su. Ya jagoran ce su cikin nasara.



A kogin Gini da ke Kwanakiri 'yan tseren suka wanke ƙurar da suka kwaso. Sai suka yanke shawarar tsere ta Maroko da Senegal da Mauritaniya.




A garin Kasabalanka 'yan tseren sun yi wasa da wasu matasa a gaɓar kogi. Daga nan, suka ci gaba zuwa tsallaken Afrika ta Arewa.




Tseren ya shiga ƙasashen Aljeriya da Libiya, sannan su ka tsaya a ƙasar Misira don ziyartar dala. Daga nan suka yi gaba zuwa gabas ta bin tekun Nilu zuwa Yuganda.



Sun ci gaba da tsere ta cikin Sahara da gandun dazuzzuka daban daban. An samu Karin matasa a garin Kampala. Gungun 'yan tseren sun nuf gaɓar kogin Kenya.



A garin Mumbasa sun zauna a gaɓar kogin inda suka ci shinkafa da Kwakwa da Kif. Tanko ya ce, "Ku zo mu dauki ftilar haɗin kan Afrirka zuwa tsaunin Kilimanjaru."




Amma Tanko ya gaji. A kan hanya zuwa Tanzaniya, ya faɗi kasa. Gaba ɗaya 'yan tseren suka dakata kuma suka juya baya domin taimakawa Tanko.




Tanko ya miƙawa Mudi ftila. Ya ce, "Ka taf da ftilar zuwa tsaunin Kilimanjaru. Ka kunna ta don haɗa kan Afrika."



Jama'a sun yi wa 'yan tseren taf, "Ku gwaraza ne." Bayan haska ftilar haɗin kai a Kilimanjaro, sai suka juyo zuwa Afrika ta Kudu.



Sun dakata domin yin ninƙaya a tafkin Malawi. Mudi ya ce wa Tanko, "Munyi tsere tun daga Kudu zuwa Arewa sannan muka sake dawowa. Yanzu tafyar mu ta ƙare."



A ƙarshe masu tseren haɗin kai sun dauki ftilar zuwa Kasar Zinbabuwe. 'Yan kallon sun taru a wannan muhimmin wuri. "Tanko yayi murmushi, ya ce tsere ke nan!"